(١)

## HAKKIN DA BAYAR DA GUDUMMUWA WAJEN GINA TA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ku shiga Misra cikin aminci da ikon Allah..)** [Yusuf: 99]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai haƙƙin da ƙasa take da shi akan 'ya'yanta yana cikin muhimman haƙƙoƙi masu matuƙar ƙarfi, bayar da gudummuwa wajen gina ƙasa, da ɗaukaka darajarta na cikin muhimman ayyuka masu daraja; ita ƙasa ɗaya ce daga cikin manya ginshiƙan Musulunci guda shida, waɗanda addininmu mai girma ya ba su cikakkiyar kariya, ɗan ƙasa mai cikakken 'yanci, da karamci shi ne wanda yake sadaukar da kansa -da ma komai da komai- wajen cigaban ƙasa, da ba ta kariya, alhairin Allah ya kai zuwa ga wanda yake cewa:

"Ƙasashe suna da daɗaɗɗen alhairi da suka gabatar wa kowane 'yantacce, suna kuma da bashi akansa"

Babu shakka duk wanda ya fahimci addininsa da kyakkyawar fahimta zai gane cewa lallai dagantaka tsakanin addini da daula ba ta taɓa zama dangantaka ce ta adawa ba, ba kuma za ta taɓa zama hakan ba, lallai fahimtar addini da kyau yana zama dalili ne da yake bayar da gudummuwa wajen gina ƙasa, da samar mata da cikakken kwanciyar hankali, ta yanda za ta yi daidai da zamani, wadda ta ginu akan ginshiƙi na mutunta ɗan ƙasa,

kaman yanda ita ma ingantacciyar daula, ba za ta taɓa cin- karo da fiɗirar ɗan Adam, wadda a koda yaushe take bincike da ƙoƙarin nemo ingantaccen imani kuma nagartacce ba.

Lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya buga babban misali na ma'anar son ƙasa, a inda (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yake cewa, lokacin da mutanensa a garin Makka suka fitar da shi daga garinsa; sai ya yi wa garin magana yana cewa: **(Wane gari ne ya kai ki daɗi, kuma wane gari ne na fi so sama da ke, ba domin mutane na sun fitar da ni daga cikinki ba, da ban zauna a ko'ina ba sai a cikinki..)**

Lallai son ƙasa ba wai kawai ya taƙaita akan kalmomin da ake yawan maimaitawa ba ne, ba kuma wani take ne da ake furtawa da baki kawai ba, shi son ƙasa tsari ne na rayuwa, da sadaukar da kai, da kuma haƙƙoƙin da mutane za su bayar da suke kansu, cikin manyan waɗannan haƙƙoƙi da suke a ƙololuwa akwai: sadaukar da kai wajen bai wa ƙasa kariya daga dukan hatsari, da barazanar da take fuskanta, wanda zai iya durƙusar da ita, ko ya sanya ta girgiza, ko ya kai zuwa ga tsoratar da 'yan ƙasa, lallai bai wa ƙasashe kariya yana cikin manyan manufofin addinai, wannan kuma aiki ne na masu daraja, da manyan mutane da masu cika alƙawurra, lallai zama ɗan ƙasa na ainihi yana nufin sadaukar da kai, da jinta a cikin zuciya, da girmama tutarta, da takenta, da sauran albarkatun da Allah ya yi mata na ma'aikatu, da manyan cibiyoyi.

Lallai kishin ƙasa na ainihi yana nufin kiyaye dukiyar al'umma, domin ita ce ginshiƙin da daula ta ginu akansu, da su take gudanar da ayyukanta, da su ne kuma cibiyoyinta suka tsaya da ƙafafuwansu, da su ne take gabatar wa 'yan ƙasa hidimomi, da manya da ƙananan ayyuka, da su ne ɗaiɗaikun mutane, da ma

al'umma suke ƙara samun ɗaukaka, suna bayar da gudummuwa wajen gina cigaba, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai mutanen da suke kutsawa cikin dukiyar Allah, ba tare da haƙƙi ba, wuta ta nan tana jiransu a ranar alƙiyama)**, lallai dukiyar al'umma ce ya fi kamata a bai wa kariya.

Lallai kishin ƙasa na ainihi yana nufin ƙarfafa kayan da ake sana'anta su a cikin ƙasa, da ƙarfafa harkokin noma, da na kasuwanci, da tallata kayanta; abin da zai ƙara sanya kishin ƙasa, da kuma soyayyarta, ya kuma tabbatar da jin daɗi na tattalin arzikin 'ya'yanta, lallai a duk sanda muka bayar da ƙoƙari wajen gabatar da aiki, da kuma kyautata aikin, sai ka ga ƙasarmu ta ƙara ƙarfi a fagen tattalin arziki, a duk sanda muka mayar da hankulanmu zuwa kayayyakin da aka samar a cikin ƙasa, ta hanyar saye, da sayarwa, gami da kasuwancinmu, za a ƙarfafi kayan da ake sana'antawa, wannan kuwa dama ce ga masu masana'antu, na su ƙara haɓaka kayansu, ta yanda za su iya yin gogayya da kayayyakin duniya, hakan kuma zai zama wata gudummuwa ce da ƙasa, da za ta kai zuwa ga samar wa 'ya'yanmu da damammakin ayyukan yi.

Haka son ƙasa yana nufin mutunta doka da oda, da tsarin shari'a a ƙasa, saboda dole ne duk al'ummar da take rayuwa a wuri ɗaya ta zama tana da wasu dokoki na adalci, da za su daidaita tsarin rayuwar mutane, su kuma kiyaye wa 'yan ƙasa haƙƙoƙinsu, kowa ya tsaya wajen sauke abubuwan da suka wajaba a kansa, idan babu irin wannan tsari, mutane ba za su taɓa iya samun haƙƙoƙinsu ba, ba za a taɓa iya tabbatar da adalci ba; lallai bin doka da oda abu ne da yake nuna wayewa, da kuma riƙo da addini, abu ne da ya zama dole wajen kiyaye ƙasa, da

tsaronta gami da kwanciyar hankalin cikinta, da samun haɓakar tattalin arziki.

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai kishin ƙasa na gaskiya yana nufin bayar da gudummuwa wajen gina ƙasa, hakan yana kasancewa ne ta hanyar kyautata ayyuka, da kuma ingata kayan da ake sana'antawa; abin da zai kai zuwa ga cigaban ƙasa, da ƙaruwar tattalin arzikin ciki, lallai addininmu mai daraja ba wai kawai yana neman mutane da su gabatar da aiki ba ne; a'a, yana neman su kyautata ayyukansu ne, su kuma inganta su, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah yana son idan kowane daga cikinku zai yi aiki to ya kyautata shi)**, tun ba yau ba ne suke cewa: Idan kana son ka san cika alƙawarin mutum, da asalinsa, da nagartarsa, da mutuncinsa; to ka duba irin yanda yake son ƙasarsa, da irin yanda yake begenta, yake kuma gabatar da aiki saboda cigabanta.

Lallai muna matuƙar buƙatar haɗa ƙarfi da ƙarfe na ɗaukacin al'umma wajen gina ƙasa; ita ƙasa mallaka ce ta dukan 'yan ƙasa, da ƙoƙarinsu da jajircewarsu da guminsu ne take iya tsayawa da ƙafafuwanta, kowa a fannin da yake aiki, da fagen da ya keɓanta da shi, soja da ɗan sanda wajen kiyaye ƙasa da ba ta kariya, da tsare tsaro, da kwanciyar hankalin cikinta, likita a asibitinsa, manomi a gonarsa, ma'aikaci a masana'antarsa, ɗalibi a ƙoƙarin

da yake yi na neman ilimi, haka ma a dukan fagagen sana'o'i da ayyuka, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Ku yi taimakekeniya wajen ayyukan alhairi, da tsoron Allah, kada ku yi taimakekeniya wajen saɓon Allah da zalunci..)** [al- Ma'ida: 2].

Ya Allah ka kiyaye mana ƙasarmu, da sauran ƙasashe baki ɗaya.